BU African Studies Center LANGUAGE PROGRAM, 232 BAY STATE ROAD, BOSTON, MA 02215 africa@bu.edu
www.bu.edu/Africa/alp 617.353.3673

# Skit 7: Hausa ba dabo ba ne

## Yazi Dogo: Wato, ita Hausa ba ta da al'ajabi, in ka koya ka iya!

| | |
|---|---|
| A: | Ka bugi **birgi** dubi ni! Ya **ishe** ni daidai! |
| B: | Yau! **Hauka** ne, ɗaki biyu hwa! Ka ce! |
| A: | Yau! Tsaya! tsaya! |
| B: | Kai **ba ka da hankali** na? |
| A: | Tsaya! Tsaya abokina. Ka gani, kai ba "maçon" ba, kai ba mai bin "maçon", ba ka taɓa **aikin gini** ba. Kuma kawai ka yi mini **gardama**. |
| B: | To! Na rance maka ko. |
| A: | **Moɗi** kake so mu yi? |
| B: | Birgi dubu ba ya tsoro. |
| A: | Ni, yanzu, na ba ka jika talatin, in dai gaskiya ne zancenka, mi ka sa, kai? Mu je mu yi moɗi. |
| B: | Ni na sa rigata |
| A: | To! Mu je, mu je dai inda za mu tambaya. |
| B: | Amma! Amma! Sai magini. |
| | - Allah! Mai yi yadda ya so |
| A: | Dan daɗi! Muna lahiya! |
| C: | Lahiya lau! Mine ne wannan? |
| B: | Birgi dubu na ce mishi, ba ya yi. |
| A: | Ɗakin ga nawa, ɗakin ga nawa na ce. Zan sa birgi dubu in tada shi, ya tashi **tsina**, in zamna. Cewa ya yi "A'a". |

© Boston University

C: A'a. Gardaman da kuke yi, birgi dubu ko suna gina, ko ba su gina.

A: E.

B: Amma! Ya sa kuɗi jika talatin.

C: Idan gina ce, za a yi daidai, birgi dubu ba uku sun isa.

A: To. Ka ji.

C: Birgi dubu ba uku sun isa.

A: Hiddo rigakka ba ni.

B: Yaya in ba ka riga?

A: Yau!

B: Na sa riga na ce.

C: Yanzu dai, ka gane, tun da ya hi ka gaskiya, sai ka ba shi riga.

B: Na sa riga fa!

C: A'a. Riga kai, ka sa?

B: Ni ni riga na sa. Kai kuɗi ka sa!

C: Ya hi ka gaskiya! Ka ba shi riga. Yanzu, ka gane ka ba shi rigarshi.

B: Yaya!

A: Kaƙa ka sa riga?

C: Ka ba shi riga!

A: Kaƙa ka sa riga?

B: Na sa riga!

C: Yau! Kai! Hausa ba dabo ba. Hausa ce ya yi ma. Yo, ya sa rigarshi.

- Wannan ɗan banza. Hausa ya iya!

- Wallahi ka halaka!

B: Yau! Ke nan, Hausa ba dabo ba, amma mutunen nan ya bugo ni. Ya yi sa'a. Lalle Hausa ba dabo ba!